# KAFIN GIDA A GARGAJIYAR HAUSAWA

**DAGA**

MUHAMMAD TAHIR RABIU
mrtahir@abu.edu.ng
SASHEN HARSUNA DA AL'ADUN AFRIKA
JAMI'AR AHMADU BELLO ZARIA

**TSAKURE**

*Kafi ko kuma tsarin gida ga al'ummar Hausawa, abu ne da aka gada tun asali, wanda sukan hi wasu hanyoyi domin samar wa kawunansu tsaro ta hanyar kafi da kuma riga-kafi a muhallansu, da wuraren sana 'o 'insu da iyali da sauransu. Wasu Hausawa sukan yi amfani da iskoki ko layu ko rataye da binne-binncn wasu abubuwa, domin tsarin gida ko gari ko gona ko iyali ko wani abu mai amfani . Ana aiwatar da haka ne domin kare mutuncin gida ta fuskar tsaro da wanin haka. Saboda haka mukalar za ta gudanar da bayani kan yadda kafiyake a gargajiyar Hausawa, da kuma hanyoyin da aka bi wajen aiwatar da shi. Wadannan hanyoyi kuwa sun hada da iskoki da hatimai,sukan yi hakan ne bisa wasu dalilai da kuma manufofi daban-daban, wadanda suka hada da tsaro ko kuma tsaren gida ko wajen sana'a da iyali da sauransu.*

## 1.0 GABATARWA

Bahaushe mutum ne da ke da tunanin cewa, kusan duk wani abu da mutum yake gudanarwa, walau na ilimi, ko sarauta ko sana'a zai tabbatar da cewa ya yi shi ba tare da an sami magabta ba. Irin wannan lamari na ganin bayan mutum a tunanin Hausawa, shi ne kusan maƙasudin sanya Hausawa wajen neman yin Kafi, domin ya kare gidansa da kuma Iyalinsa, sai dai irin wannan Kafi kan taimaka wajen karegidadaga kowane irin haɗari na mutum ko na Iskoki da sauransu.

Wani lokaci Hausawa kan yi Kafi ne, domin jawo alhairi a gidansu, musamman yadda suke mu'amala da ma'abota Iskoki ko 'yan bori da sauransu.Sukan yi hakan ne domin samun ƙarfin gwiwar aiwatar da Kafi na gida wajen jawo alhairi, musamman jama'ar da ke gidan waɗanda wannan alhairin zai sama.

Kafi na iya zama wata hanya da Hausawa ke bi wajen kare muhalli ko iyali ko wurin sana'a da sauransu. Yinkafi ga dukkan wani lamari, yana nuna cewa mai mallakar wannan gida ko gona ko Iyali tsayayye ne. Hausawa a gargajiyance na ɗaukar mai gidan da ya kasa kafe gidansa ko wasu abubuwan da aka yi bayaninsu a matsayin namiji rago.

Saboda haka kafi a gargajiyar Hausawa wata hanya ce ta nuna bajinta, da nuna tsayawa kan abubuwan da mutum ya mallaka, domin guje wa halakarsu ko kuma keta masa alfarma. Ke nan kafi wani tsari ne, wanda Hausawa ke togo da shi wajen kariya dangane da abubuwan da yake da iko da su da kuma wanda ya mallaka.

Irin wannan halin kula da Hausawa ke da shi, kusan hakan ya jawo hankalin wannan muƙala ta yi bayanin wasu daga cikin nau'o'i na kafin da Hausawa ke da shi, dangane da tattalin rayuwar al'ummarsa da kuma abin da ya mallaka na muhalli da Iyali da sauransu.Wani lokaci ma Hausawa kan yi Kafi a harkokin sana'a.

## 2.1 KAFIN GIDA

Kafin-gida na nufin tsare muhalli ko iyali ko gida ko wurin sana'a, domin kare mutuncin wannan abu, tare da bin wata tsararriyar hanyar da wannan al'umma ta aminta da ita.

Ko da yake Kalmar kafin gida, kalma ce wadda take guda biyu, kafi da kuma gida waɗanda kowannen su yana da ma'ana kamar haka; kafi na nufin sanya wani abu da nufin kare wata dukiya ko wasu kaya daga cutarwa.

Shi kuwa gida na nufin dukkan wani gini da wani ko wasu za su iya zama a cikinsa, musamman wanda yake da wasu ɗakuna domin amfanin iyali Domin wasu na gani ai kafi ko tsaro ba wai kawai ya tsaya ne, ga kare muhalli kawai ba, daga ɓarayi ko kuma wani mai cutarwa, kusan a iya cewa tsaro na nufi duk wata kariya da za a ba mutum wacce ta danganci tun daga abinci har zuwa yanayi mai kyau domin samun rayuwa mai inganci da sauransu. (Nwolise, 1988).

ɗan adam na buƙatar muhimman abubuwan rayuwa musamman waɗanda suke buƙatar kulawa, domin da su ne mutum ke fafutukar biyan buƙata, sai dai idan aka tsare masa muhimman abubuwan buƙatar na yau da kullum tun daga muhalli da tsaro da sauransu sai a sami damar yi masa cikakkiyar tarbiyya gwargwadan hali. (Umar. 1987).

Wasu na ɗaukar kafi a matsayin wata hanyar da za su iya tsare kowane irin abu da suke buƙata, walau ta hanyar son abin kamar matar mutum ko kuma gida ko gona da sauran, Hausawa da yawa sun aminta da wannan al'ada ta kafi.

Idan Bahaushe na son matarsa ta tabbata gidansa komai wahalar da yake ba ta, ko yana son ya tsare gonarsa, ko gidansa, ko yana son ya hana wata cuta da suka gada a gidansu, ta sake tashi zai yi kafi. Akwai kahin gari, na hana cin garin da yaƙi. Sannan akwai kafin kuturta wanda ake hana ta yaɗu,

akan yi kahi da mahaɗai kamar kayan tsafi ko turbuɗe wani abu a wurin da ake son yin kahin…………(Bunza, 2006).

Saboda haka wannan ya nuna cewa Bahaushe ya yi imani da wannan al'ada ta kafi domin cim ma wata manufa tasu, a cikin iyali ne ko kuma a gidansa ne, ko kuma gona.Ya danganta da yadda yake son aiwatara da wannan kafin.

## 2.2 RABE-RABEN KAFIN GIDA

Kafin-Gida ya rabu zuwa kashi biyu kamar haka:

i. kafi na hatimai.

ii. Kafi na iskoki.

### 2.2.1 Kafin Hatimai

Shi ne kafin da ake aiwatar da shi da abubuwan da suka shafi ayoyi ko wani taimako da nufin tsare gida da abin da ya shafe shi, sau da yawa akan yi kafin gida da hatimi sannan a haɗa da sauran kayyayyakin haɗi kamar su ƙahon rago ko na akuya ko ƙankon dodon-koɗi. waɗanda suka danganci wannan kafin. Akan yi tunanin cewa shin kafe mace za a yi ko kuwa gida ne, ko kuwa jawo wani alhairi ake so. Wani lokaci akan yi kafi da hatimi a rubuta a takarda a naɗe kamar laya, sannan a haɗa ko da ƙaho ko kuma a sanya layun a cikin ƙwalba, sai a rataye a zaure ko kuma idan na binnewa ne sai a binne walau a cikin ginin gidan ko kuma a tsakiyar gida ko kuma a ƙarƙashin murhun da ake girki da dai sauransu. Hira (Muhammad, 2013: 10:08pm)

### 2.2.2 Kafi Na Iskoki

Iskokin da ake amfani da su domin yin kafin gida, su ne :

i. Mai-dawa

ii. Danko

iii. Bagiro ko Magiro

i. **Maidawa** :-Iska ce wadda aka fi amfani da ita wajen kafin gida, sai dai Maidawa suna da yawa a tsarin iskoki, wanda aka fi amfani shi cikin su shi ne, Maidawa Adam wanda ake yi masa yanka da kaza durgu, shi wannan Maidawa bafilatani ne, sannan kuma ya fi hulɗa a daji, har wasu ma na yi masa kirari da cewa ''Dawa kan gidansu''. A lokaci da ake gudanar da kafi da iska Mai-dawa sau da yawa ana ganin kayan Mai-dawa a kafe a gidankamar gatari da sauran kayansa, waɗanda ake haɗa irin wannan kafi da su, sannan kowane lokaci kuma yana nan yana kula da wannan gida dangane da abin da ake buƙata a wurinsa.

ii. **Danko** :- Iska ce wadda ake kira da bakan-gizo, wanda yake shiga cikin rijiya, sannan danko kusan su biyu ne, domin yana da ɗanuwa mai suna

Inusa shi ne ɗan inna, wanda yana zama maciji mai jan ciki, shi kuwa ɗaya watau Musa shi ne yake a rigingine yake tafiya, sau da yawa yakan shafi maciji sai a ce maciji ya koma danko, musamman idan macijin ya daɗe ya manyanta, a kan yi kafin gida da shi, da ɗabi'unsa da abubuwan da yake buƙata na yanke-yanke, amma a ɓangare kafin gida, musamman wani lokaci kyautar ƙuli da sauran kayan da yake buƙata domin yak are wannan gida a matsayin kafi.

iii. **Bagiro** :- Wani babba ne, a cikin kusan kafiran iskoki, a kan yi amfani da shi a ɓangaren kafin gida, shi ta hanyar yi masa yanka da abubuwan da yake buƙata, domin kafin gida. Hira : (Hamisu, M. 2013 ; 11 : 46PM)

Wannan kafi yana taka muhimmiyar rawa ne, wajen samun natsuwa ga duk wanda ya zamo yana da irin wannan nau'in a gidansa, haka kuma da yawa daga al'ummar Hausawa su na amfani da wannan hanya ce domin samun natsuwa dangane da abokan gaba ko kuma magabta. Wani lokaci irin wannan kafi yana ba da ƙwarin gwiwa dangane da, dangantakar al'umma da iskoki, musamamn wajen ƙara yarda da kuma jaddada miƙa wuya ga iskoki. Sannan duk da zuwan musulunci bai hana wasu daga cikin al'ummar Hausawa amfani da wannan hanya ba.

## 1.3 IRE-IREN KAFIN GIDA

Akwai nau'o'in kafin gida da Hausawa ke da su. Akan aiwatar da kafi ne a bisa dalilai da manufofi daban-daban kamar haka:

- Kafin gida domin maganin ɓarawo
- Kafi domin tsare mace daga fita ko kashe aure
- Kafin gida domin cutarwar daga iskoki
- Kafi domin abokan gaba ko maƙiya
- Kafin jawo alhairi ko arziki

### 1.3.1 KAFIN GIDA DOMIN MAGANIN ƁARAWO

Irin wannan kafin gida ana yinsa ne da nufin maganin ɓarayi, domin hana su shiga wannan gidan, ko a kaucewa ɓarnarsu. A irin wannan kafi akan yi amfani ne da hatimai gwargwadon wanda mutum yake da shi.

Idan har an sami nasarar aiwatar da wanan kafi, yakan sa ɓarawo ganin abubuwa da dama, waɗanda kuma sukan iya tsoratar da shi, musamman idan ya nemi shiga wannan gidan ko tsallakawa.Yana iya haɗuwa da abubuwa kamar haka:

i zai ga zaki ya taso masa baki buɗe zai cinye shi.
ii ko gidan ya zama ƙaton kogi mara iyaka.
iii ko gidan ya zama ƙungurmin daji mai sarƙaƙiya.

iv ko gidan ya zama wata wuta mai ci ganga-ganga.

v ko gidan ya koma ƙaton dutse mai wahalar hawa.

Waɗannan a sauran abubuwan masu ba da tsoro ainun, sukan sa daga ƙarshe dole ɓarawon ya haƙura daga niyarsa ta shiga wannan gida.

Ko da yake a wasu wurare akan aiwatar da kafin gidan ne, a bakin ƙofar gida, wanda wasu ke sanya layu tare da ƙaho ko kuma ƙoƙo cike da layu a rataye a ƙofar gida da sauransu. wasu kuwa sukan binne kafinsu ne, a ƙasa ko a tsakiyar gida ko kuma a kusurwar gidan guda huɗu, ku kuma lokacin sanya fandisho sai a haɗa a cikin gini gaba ɗaya.

Saboda haka ga samfurin wasu hatimai da ake kafin gida da su, domin hana ɓarawo shiga gida ta kowace fuska:

## 1.3.2 KAFI DOMIN TSARE MACE

Kafin tsare mace yana daga cikin ire-iren kafin da al'ummar Hausawa ke yi, domin su kafe mace daga fita daga gidan miji ko da kuwa ana gallaza-mata, Idan Bahaushe ya ga ana wahalar da mata, amma ba ta nuna barazanar fita gidan ba, yakan ce, " kai abu kamar wadda aka yi wa kafi a gidan" (Bunza 2006)

Wannan kafi da al'ummar Hausawa ke aiwatarwa yana hana mace yawan fita anguwa barkatai da sauran yawace-yawace marasa dalili. Haka kuma, irin wannan kafi na taimakawa wajen rage mutuwar aure, ko da kuwa ana gallazawa matar.

Bahaushe yana wata fahimta, ko tunanin cewa mutuwar auren 'ya mace na ɗaya daga cikin alamun nuna cewa maigida wannan mata, ba tsayayyen mutum ba ne a cikin gidansa, ta kowace fuska walau ciyarwa ko waninsa. Wato mutuwar aure na nuna cewa wannan maigida baya iya ba da umurni a gidansa abi. Hakan na fassarawa al'umma cewa duk wanda zai auri 'yar irin wannan maigida, to yasan cewa ya auri 'yar mutumin da ba tsayayye ba domin ya kasa tsare gidansa.

Haka kuma wani lokaci maza kan aiwatar da kafin tsare mace ne, domin su yi tasiri ga duk al'amuran matayensu, saboda duk irin bacin rai da zata shiga, cin mutumci da sauransu na saɓanin yau da gobe, wannan mata ba za ta yi tunanin wai bari ta fita ba, ko da kuwa ta yi yaji ne.

Saboda haka Hausawa na aiwatar da wannan kafi ne, a cikin gidajensu domin magance irin waɗancan matsaloli. Irin wannan al'ada ta kafi na tsare mace a gida, a mafi yawa akan aiwatar da shi ne, a cikin gidan da matar take.Wasu kuma sukan yi hakan tun kafin su yi auren; wasu kuwa sai ta zo an ga irin nata halin.

## 1.3.3 KAFIN GIDA DOMIN CUTARWA DAGA ISKOKI

Bahaushe mutum ne wanda ya amince da Iskoki, ko aljanu ko ƙwanƙwamai ko mutanen ɓoye. Iskoki wata halitta ce, kamar sauran halittu, sai daisun sha bamban ta fuskar tsarin su, da ƙirarsu, da mu'amalarsu ta yau da kullum.Da canza halinsu da sarrafa jikinsu, sannan ba a iya ganin su da ƙwayar ido. (Bunza, 2006)

Hausawa na yi wa gida kafi domin kariya daga iskoki, musamman ganin yadda Hausawa su ka yi imani da su, hakan ya sa wasu Hausawa ke ganin ana iya samun cutarwa daga cikin iskoki na iya cutar da al'umma, a tunanin Hausawa wasu na ganin duk wata cuta ko annoba, da ta sami mutum to dole a kwai tasirin iskoki a dangane da faruwar lamari.

A Bahaushen imani na gargajiya, kowace irin cuta ta cikin jikin mutumdole tana da mafari, musamman Hausawa sun keɓe wasu cutuka waɗanda suke ganin cewa daga iskoki ne, domin cutar da ake ganin iskoki ne masabbabinta aukuwar tasai masana iskoki za a bar wa irin wannan cutuka…
(Bunza, 2006)

Ana yin kafin gida dangane da cutar da ake gudu daga iskoki, musamman cutuka kamar irin su :

- Cutar shan inna, da Surutai cikin dare, da Daka cikin dare a gida
- Ciwon mutuwar gaba da Karayar arziki, da sauran su

Saboda haka, Bahaushe kan sanya kafin gida, domin neman tsari daga kowace irin tasirin da iskoki ke iya haddasawa a wannan gida, walau an turo su ne, ko kuma hanya ce ta haɗa su da gidan. Haka kuma irin wannan kafi na iskoki shi ma, a kan binne ne, a cikin gidan ko kuma a rataye a wani wuri a cikin gidan da sauransu kamar ƙofar ɗaki ko tsakiyar gida ko inda ake daka a cikin gida ko gefen rijiyar gida.

## 1.3.4 KAFIN GIDA DOMIN ABOKAN GABA KO MA{IYA

Hausawa na tunanin cewa a kowane irin lamari na rayuwa, mutum baya rasa magabci, na kusa ko na nesa, wanda yake tunani yana iya cutar da shi a kowane irin lamari idan ya yi sakaci.Da yawa wasu ke hana idansu barci ko kuma su kasa zaune ko tsaye domin ƙwafagwalom ganin sai sun ga bayan mutum.

Har wa yau, irin wannan neman ganin bayan mutum, kan sanya Bahushe neman yadda zai yi, ya yi kafin domin irin waɗannan mutane, wajen kare kansa da gidansa da iyalinsa, kai har ma da sana'arsa.(Abdullahi, 2000)
Akan yi irin wannan kafi domin kare kai daga kowane irin jifa, da za a jefo a wannan gida ko kuma iyalin wannan gida. Irin wannan kafi wasu sukan sanya

shi ne, a wajen gida wasu kuma sukan binne kafin ne a cikin gida, wasu kuma a inda suka ga ya dace.

### 1.3.5 KAFIN GIDA NA JAWO ALHERI A GIDA

Bahaushe mutum ne, mai son ya sami sa a, a kowane irin lamari da yasa gaba, sannan kuma yana da ƙoƙarin mu'amala da 'yan bori, da sauran su, wani lokaci kuma yakan so yasan abin da zai je ya komo.Kusan hakan ce kan sanya shi zuwa neman abin da yake ganin ko tunanin yin su zai kawo masa samu, walau a harkar kasuwa ne ko kuma wanin haka. (Abdussalam, 1986)

Irin waɗannan dalilai su ne, ke haddasa samun karfin gwaiwar neman kafin jawo alhairi ga gida ko ayalin gidan, kamar haka:

- Kafin maganin farin jini ga 'ya'ya mata dake gidan.
- Kafin maganin kwarjini ko nuna isa domin jama'ar gidan.
- Kafin hana galaba ga mutanen gidan.

### 1.4 ABUBUWAN DA AKE AMFANI DA SU A KAFIN GIDA

Ana amfani da abubuwa da dama wajen haɗa ire-iren kafin gida, duk da cewa kowane kafi yana da na sa keɓaɓɓun kayan da ake buƙata wajen haɗin kafin gidan.

Saboda haka ga misalin wasu daga cikin kayyayakin da ake buƙata don aiwatar da kafin gida ;

- {aho na baƙin rago ko fari ko akuya, ko dodon-koɗi.
- Baƙin zare ko fari ko kuma abawa
- Saƙi, fari ko baƙi.
- Kwalba, da Alƙalami, da Auduga, da Takarda, da Turaren-juda, da Fata, da Wuri, da Allo na ƙirya ko na ƙarfe, da Gatarin aradu, da sauransu.

Waɗannan abubuwa da aka zayyano da waɗanda ba a zayyano ba, kusan suna daga cikin abubuwan da ake nema wajen haɗa kafin gida.

### 1.5 DALILAN YIN KAFIN GIDA

Kowane abu kusan baya rasa dalilai dake sanya a aiwatar da shi. Saboda haka, dalilan dake haifar da kafin gida ba sa wuce neman zaman lafiya, ba tare da wani ya matsawa wani ba, ko da kuwa wannan mutum mugu ne.dangane da haka dalilan yin kafin gida sun haɗa da:

i. A sami tsaro da kare mutuncin gida.
ii. Kare gida daga annoba kowace iri.
iii. Jawo alhairi ga ahalin gida.
iɓ. Samawa kai zaman lafiya tare da iyali.
ɓ. Samun damar mallakar gida da abin da ya ƙunsa.
ɓi. Shimfiɗa iko ba tare da tsangwama ba.